# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Al'ajiban Yesu



Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Byron Unger; Lazarus
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter; Sarah S.

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2023 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.

Yesu ya yi al'ajibai masu yawa. Al'ajibai alamu ne masu nuna cewa Yesu shi Dan Allah ne. Abin al'ajibi na farko ya faru ne a bikin aure. Damuwa ta taso. Babu isashen ruwan inabi ga kowa.



Maryamu, mahaifiyar Yesu, ta gaya masa damuwan, sai ta gaya wa masu hidimar su yi duk abin da Yesu ya umarce su.



“Ku cika tukwanen nan da ruwa,” Yesu ya ce. “Ruwa?” watakila sun tambaya. I’I, ruwa ne abin da Yesu ya tambaye su.



Sa’an nan Yesu ya gaya wa daya daga ‘yan hidima ya diba daga babban tukunyan ya ba wa mai gudanar da bikin ya taba ya ji yadda yake.  Yanzu ruwan ya zama ruwan inabi! Ruwan inabi mai kyau! Mafi kyau na ruwan inabi!



Masu hidimar suka yi mamaki. Yesu ya canja ruwa zuwa ruwan inabi.  Allah kadai zai iya yin wanan al’ajiban.



Yesu ya aikata wadansu al'ajibai. Wani yamma, da shi da almajiransa suka je gidan Bitrus.  Surukin Bitrus tana fama da zazzabi.



**Yesu ya taba hannun mace mai zazzabin. A dan lokaci sai ta warke. Sai ta tashi domin ta yi wa Yesu hidima da shi da almajiransa.**



Ya zama kamar duka mutanen birnin sun tattaru a kofar gidan da yamman nan.  Marasa lafiya suka zo – makaho, kurma, bebe, da gurgu.  Har ma da wadanda aljanu na zama a cikinsu suka kewaye Yesu.  Zai iya taimakon mutane da yawa haka?



Yesu, Dan Allah, zai iya taimako. Kuma Yesu ya taimaka. Duka wadanda suka zo gareshi, an warkar da su. Masu rayuwa da sandunan tafiya sun iya tafiya da gudu da tsalle.



**Wadansu sun zo, wadanda kuturta ya lallace musu fuska.**



Sun zama
lafiyayyu kuma
tsabtsab sa’ad
da Yesu ya
warkar
da su.



Maza da mata masu fama da aljanu suka tsaya a gaban Yesu. Ya ba da umarni aljanun su bar su. Yayinda aljanun suna biyayya, suna tsoro, marasa murna sun kasance cikin natsuwa da farin ciki.



**A bayan taron jama'a, maza hudu sun yi kokari su taimaki abokinsu domin ya kai wurin Yesu. Amma ba su iya kai kusa ba. Mene ne za su iya yi?**



Suka dauki mara lafiyan zuwa kan ginin gidan, wadannan abokan kirki suka balle kan dakin suka saukar da shi a ciki. Yanzu ya yi kusa da Yesu.



Yesu ya ga cewa abokan nan hudu suna da bangaskiya. Sai ya ce wa mara lafiyan, "An yafe zunubanka. Dauki gadonka ka yi tafiya." Mutumin ya tashi, da lafiya da karfi. Yesu ya warkar da shi.



Ba a dadde ba, Yesu yana tare da almajiransa a jirgin ruwa. Sai hadari mai ban tsoro ya bullo a tekun. Yesu yana barci. Almajirai masu tsoro suka tashe shi. "Ubangiji, ka cece mu," suna ihu. "Mun halaka!"



“Tsaya cik,” Yesu ya umarci taguwar ruwan. Nan da nan tekun ya tsaya cik. “Wane irin mutum ne wannan?” Almajiransa suna tambaya. Har ma iska da teku suna yi masa biyayya.



Sun badagaskiya cewa Yesu Dan Allah ne saboda irin ayyukan al’ajibin sa suna nuna daukakarsa. Almajiran ba su sani ba, amma za su yi ta ganin yadda Yesu yake aikata abububuwa masu ban mamaki



yayinda yake yi wa Allah hidima a tsakanin mutane.

# Al’ajiban Yesu

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Matiyu 8-9, Markus 1-2, Markus 4,
Luka 4, Luka 8, Yohanna 2

“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130

**KARSHE**

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da
wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da
zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki
kuma ka yi magana da Allah a kulla
yaumin. Yahaya 3:16